**GONI**: **MAJALLAR ILIMIN ALKUR'ANI** **الغوني: مجلر علمن القرآن**

Cibiyar Nazari akan Alkur'ani da ke Jami'ar Bayero ta Kano, ta kudurta wallafa Majalla da harshen Hausa wadda musamman za ta dukufa wajen hidima ga ilimin Alkur'ani. Majallar za ta gabatar da bincike da bayanai da labarai da suka shafi fannonin ilimin Alkur'ani. Manufar Majallar ita ce samar da wani dandali da malaman Alkur'ani za su baje kolin ilimin Alkur'ani domin kusantar da fahimtarsa ga al'umma.

Majallar za ta zakulo ababen alfaharinmu na tarihin ilimin Alkur'ani a wannan kasa, musamman fannonin iliminsa da malaman wannan kasa suka yi fice a kai. Don haka za ta fuskantar da bayanai akan kafuwar makarantun tsangaya da yaduwar ilimin Alkur'ani da tarihin fitattun Alaranmomi da Gwanaye na da da na yanzu da yanayin tsare-tsarensu wajen habaka koyon karatun Alkur'ani. Majallar za ta kuma yi kokarin fayyace bayanai na malamai da masana akan hanyoyin da suka dace a bi domin habaka makarantun Alkur'ani da tsangayu da inganta manhajarsu domin dacewa da muhimman bukatun al'ummar musulmi a yau.

Majallar Al-Goni za ta kunshi bayanai da labarai na ayyukan Cibiyar Bincike akan Alkur'ani da sauran cibiyoyi da makarantun Alkur'ani.

**Harshen Majalla**: Za a buga Majallar da harshen Hausa a rubutun ajami da kuma boko.

**Bukatar makaloli**: Majallar ta na gayyatar kwararrun malamai da ma dalibai akan su aiko da makaloli na ilimi da bincike mai zurfi akan Alkur'ani mai girma domin wallafawa a wannan Majalla ta Alaranmomi da masu sha'awar karatun Alkur'ani.

Dukkan Makala ta ilimi da aka aiko, za a mika ta ga kwararrun malamai biyu don su yi muraja'arta da bayar da shawara akan dacewartata fuskar

ilimin da ta kunsa da ka'idodin rubutu da alakar makalar da fannin ilimin Alkur'ani.

**Sassan Majalla**: Majallar Al-Goni za ta kunshi sassa guda uku;

1. Sashen Makaloli da bincike na ilimi mai zurfi.
2. Sashen bitar littafan tafsiri da fannonin ilimin Alkur'ani.
3. Sashen bayanai da labarai akan cibiyoyi da makarantu da al'amura da suka danganci Alkur'ani.

**Tsarin gabatar da Makala**: Ana bukatar ko wacce Makala a shafinta na farko ta kunshi sunan marubuci da cikakken adireshinsa da maudu'in Makalar.

Ana bukata da farko a bayar da kanun bayanin da Makalar ta kunsa a cikin kalmomi takaitattu da basu wuce 200 ba.

Tsawon Makala ka da ya wuce shafi 15 a takardar A4 tare da bayanin littafan da aka nakalto bayanai daga cikinsu.

Makalar da ta gaza akan wassu sharuddan da aka ambata amma aka ga dacewarta ta wassu bangarori dabam, to za a iya buga ta a sashen bayanai da labarai.

Ana iya aiko da Makaloli ta adireshin Majalla da ke kasa:

Edita,
Al-Goni: Majallar Ilimin Alkur'ani,
Centre for Qur'anic Studies,
Bayero University, Kano

**Editorial Board:**

Editor-in-Chief

Prof. Ibrahim Muhammad

Editorial Board

| | |
|---|---|
| Dr. Goni Aliyu Haruna | Editor |
| Dr. Tijjani Zubairu Rabi'u | Managing Editor |
| Dr. Yahaya Goni Yahuza D/Zaraga | Business Manager |
| Dr Nura Sani | Member |
| Dr Yakubu Magaji | Member |
| Mal. Shuaibu M. Shuaibu | Secretary |

**Editorial Advisors**

Prof. Dandatti Abdulkadir

Prof. Hafizu Miko Yakasai

Prof. Sa'idu Muhammad Gusau

Alaranmma Goni Yahuza DanZarga

Alaranmma Goni Dan-Almajir